



An yi wasu ƙannu biyu da ake kira Halima da Fatuma. Uwayensu sun rasu. Yan matan biyu suna rayuwa a wani yanki mai hamada. Ba ruwan sama, ba cimaka. Kowa yake son abincin, sai ya yi tafiya mai nisan gaske.



18/02/2022 11:44



Halima yarin ce ma ɗa'a, lafiya da kuma kirki. Kanwarta Fatuma tana son rayuwa kuma ba ta jin gargaɗi. Ba ta kula da sauran mutane kuma ba ta darajjanta su.



Wata rana, ƙannuwan biyu sun tashi daga barci, kuma sun fiskanci cewa babu abinci ko kaɗan. Sai suka yi niyyar tafiya neman abincin. Halima da Fatuma sun ɗauki hanya dabam-dabam.



18/02/2022 11:44



Lokacin nan, wata tsofuwa da ake kira Amina tana rayuwa kusa da gari. Tana da ƙoƙarin temakawa don tana da arzika. Sai dai Amina tana da kuturta, kuma duk jikinta ƙuraje ne.



Yarinyar_Da_Ta_Yi_Arziki.pdf 6



Fatuma ta haɗu da wannan tsofuyar, da ta kiraye ta "Ɗiyata, kina lafiya? Daga ina kike? Ina za ki?"



18/02/2022 11:44



Fatuma ta amsa duk tambayoyin. Bayan haka, sai tsofuwar matar ta ce, "Maida ni gidana, kuma zan gaya miki abin da za ki yi." Fatuma ta wulaƙanta tsofuyar. Ta ce mata: "Na fi son in mutu da taɓa wannan ƙurajen naki."



Tsofuwar ba ta ce komi kuma ta mata fatan ta sabka lafiya.



18/02/2022 11:44



Fatuma ta yi ta tafiya har sai da ta zo wani wuri na mamaki. Wurin akwa shanshani, macizai, kai da duk wani ƙwari. Fatuma ta gaji, kuma ga yunwa saboda ba ta ci komi ba. Ko da ta zamna ta futa, sai ƙwarin suka fito suka cinye ta.



Bisan hanyarta, Halima ita ma ta haɗu da tsofuwar. Ta yi farin cikin ganin Amina, saboda ita ce mutum ta farko da ta haɗu da ita cikin wannan bulaguron. Tsofuwar ta kiranyo ta kuma ta muta tambayoyi kamar yadda ta yi ma yar uwarta.



18/02/2022 11:44



Fatuma ta yarda ta maida tsofuwar gidanta. "Kin yi aikin da mutane da yawa suka guje ma," in ji tsofuwar. Sai ta ba ma Fatuma wata sanda kuma ta ce mata ta koma gida, can za ta iske duk abin da take so.




Yarinyar_Da_Ta_Yi_Arziki.pdf 5



Fatuma ta gode ma tsofuwar sosai kuma ta yi gaugawa ta koma gida. Ta tarda a gidan, ɗaki cike da kaya da abincin. Ta zamanto itace ma arzikin garin.



18/02/2022 11:44



Amma ta yi ta kuka da rishin
ƙanwarta kuma ta ce, "wandan bai jin
gargaɗi zai gamu da mugun abu."